# Lallai mafi ƙiyayyar mutane a wurin Allah (shi ne) mai taurin kai mai tsananin husuma

Daga A'isha - Allah Ya yarda da ita - daga Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a greshi - ya ce: "Lallai mafi ƙiyayyar mutane a wurin Allah (shi ne) mai taurin kai mai tsananin husuma".
[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi - yana ba da labarin cewa Allah - Mai girma da ɗaukaka - yana ƙin mai tsananin husuma, kuma mai yawaitata daga cikin mutane, wanda ba ya karɓar jawuwa ga gaskiya, kuma yana ƙoƙarin tunkuɗeta da jayayyarsa, ko ya yi husuma da gaskiya, sai dai cewa yana kai matuƙa a cikin husuma, kuma yana fita daga iyakar daidaituwa, yana jayayya ba tare da ilimi ba.



النجاة الخيرية
ALNAJAT CHARITY
لجنة الدعوة الإلكترونية
EDC E-Da'wah Committee